# MU SO JUNA

## WASIKA ZUWA GA MUSULMI DAGA WAZIRIN KATSINA KAN MUHIMMANCIN SON JUNA DAGA AYOYIN AL-KUR'ANI DA HADISSAI

**Na**
**WAZIRIN KATSINA Na 5**
**Prof. Sani Abubakar Lugga, MFR**

**By:**
**Professor Sani Abubakar Lugga, MFR**
**The 5th Waziri of Katsina**
**Professor of Management Studies**
**Doctor of Philosophy in Conflict Management**
**Fellow of the Nigerian Institute of Management**
**Fellow of the Institute of Management Consultants (Nigeria)**
**Fellow of the Institute of Professional Financial Managers (UK)**
**Fellow of the London Graduate School, London, United Kingdom**
**Key Founder and former Senior Lecturer, Al-Qalam University, Katsina**
**Visiting Prof., Ecole Superieure Universitaire, Cotonou, Benin Republic**
**Visiting Professor at St. Clements Private Swiss University, Switzerland**
**Committee Member, Nigeria Supreme Council for Islamic Affairs**
**Committee Chairman, Jama'atuNasril Islam, Kaduna, Nigeria**
**Member of Sultan Foundation for Peace and Development**
**Executive Member, Interfaith Initiative for Peace, Nigeria**
**Ambassador of Universal Peace Federation, New York**
**Member of Professors World Peace Academy, Korea**

**www.books.luggaweb.com**

**Haƙƙin Mallaka © Prof. Sani Abubakar Lugga**
**© Copyright: Prof. Sani Abubakar Lugga**

**Ɗab'in Maɗaba'ar Lugga**
**Gidan Lugga, Titin Kofar Marusa, Katsina,**
**Jihar Katsina, Najeriya.**

**An Fara Wallafawa Da Bugawa:**
**Jumada Ula 1426 Hijra (June 2005)**

**An Sake Bugawa:**
**Rajab 1436 Hijra (May 2015)**

بسم الله الرحمن الرحيم.
نحمده تعالي ونشكره علي نعمه والصلاة والسلام علي
رسوله الكريم وعلي آله وصحبه أجمعين.

## Zuwa ga ‘Yan Uwana Musulmi,

Da sunan Allah Mai Rahama Mai Jinƙai. Dukkan godiya ta tabbata ga Allah Maɗaukaki wanda muke gode mawa domin ni’imomin da ya yi mana. Tsira da Amincin Allah sun tabbata ga Manzon Allah, Annabi Muhammadu, da Alayensa da Sahabbansa.

Assalamu Alaikum,

Na yi wannan wasiƙa zuwa ga dukkan ‘yan-uwa Musulmi domin damuwa da irin yadda muka rar-rabu muka watsar da son juna muka bada damar da aka danne mu. Masu hikima cikin Hausawa su kan ce:-

*Sai bango ya tsage ƙadangare ke samun wurin shiga.*

Mai Martaba Sarkin Katsina, Alhaji Muhammadu Kabir Usman yakan gyara wannan magana ta masu hikima da cewa sabo da girman tsagar da bangon mu ya yi a yanzu kada ma ke shigewa ba ƙadangare ba!

To, abin fahimta dai anan shine, bangon Musulmi ya tsage kuma ƙadangaru ko kadoji sun shiga sun hana mu walawa. Ashe ya zama tilas mu gyara bangon mu idan dai muna son cin amfaninsa.

Wasiƙa kamar wannan ba zata yiwu ba ga Al-Majiri kamar ni, sai da gudummuwa daga Malamai. Don haka nike miƙa godiya ta ga Malamai na wadanda suka duba wannan wasiƙa kuma suka bada shawarwari da kuma waɗanda ni kan nemi ilmi wajensu. Malaman sun hada da Liman Abba Muhammad Aliyu, Sheik Abubakar Ibrahim Charanci, Ustaz Labaran Imam Saulawa da Ustaz Muhammad Sagir Adam. Muna bukatar duk wanda ya ga kuskure a wannan wasiƙa to don Allah ya gyara kuma ya aiko mana domin mu ma mu gyara.

Muna roƙon Allah (SWT) Ya sanya albarka ga wannan aiki, Ya yi mana gafarar kura-kuran mu kuma Ya sanya mu cika da imani idan ajalin mu ya zo, ameen.

## Muƙaddima

Ya 'yan-uwana Musulmi, zan ɗauka cewa dukkan Musulmi ya karanci littafin nan na hadissan Manzon Allah (SAW) guda arba'in, watau "Arba-una Hadith" tun yana ɗan yaro. Hadisi na farko yana Magana ne akan cewa an gina ayyukan mutum bisa irin niyyar da ya yi. Hadisi na biyu yana bayyana mana cewa MUSULUNCI shine shaidawa babu abin bauta mawa da gaskiya sai Allah (SWT) kuma Annabi Muhammadu (SAW) Manzon Allah ne. Sannan mutum ya yi Sallah, ya bayar da Zakka, ya yi Azumin watan Ramadhan kuma ya yi Hajji idan yana da hali.

Manzon Allah (SAW) ya ci gaba da bayani a cikin wannan hadisi na biyu da cewa IMANI shine bada gaskiya da Allah da Mala'ikunSa da LitattafanSa da ManzanninSa da Ranar Lahira, har zuwa ƙarshen hadisin.

Ashe Musulunci baya tabbata sai da Imani kuma shi Imani baya cika sai da son juna kamar yadda Annabi (SAW) ya bayyana mana. An karɓo daga Anas bin Malik (RA) wanda shi mai yi ma Annabi (SAW) hidima ne kuma Bukhari da Muslim suka ruwaito, cewa, Manzon Allah (SAW) ya ce:-

**لا يؤمن أحد كم حتى يحب لأخيه ما يحب لنفسه**

*Ɗayan ku ba zai zama mai cikakken Imani ba sai ya so ma ɗan-uwansa abinda yake so ma kansa.* (Hadisi na 13 a Arba-una Hadith).

Ya 'yan-uwana Musulmi, mu lura cewa sai mun so juna ne zamu zama masu cikakken imani. Don haka mu yi ma kawunan mu waɗannan tambayoyi:-

1. Wane mai mulkin siyasa ko sarauta ne ke son ɗan-uwansa shi ma shi samu?
2. Wane attajiri ne ke son ɗan-uwansa shima ya zama attajiri?
3. Wane malami ne ke son ɗan-uwansa shima ya zama malami?

Kai, abin da wuya, amma fa tilas ne domin Manzon Allah (SAW) ya hore mu da muyi haka. Da mai mulki ko sarauta

ko arziki ko ilmi zai daure ya so ma ɗan-uwansa waɗan nan abubuwa da yake so ma kansa, to sai ka ga Allah (SWT) cikin hikimarsa da ikonsa da falalarsa, Ya sanya dukkan su sun samu abin kuma ba da wanin su ya rasa nasa ba. Mu duba labarin da Allah Ya bamu na Annabi Musa (AS) da ɗan-uwansa Annabi Haruna (AS) mu gani. Allah (SWT) Ya ce:-

وَٱجْعَل لِّى وَزِيرًا مِّنْ أَهْلِى ﴿٢٩﴾ هَٰرُونَ أَخِى ﴿٣٠﴾ ٱشْدُدْ بِهِۦٓ أَزْرِى
﴿٣١﴾ وَأَشْرِكْهُ فِىٓ أَمْرِى ﴿٣٢﴾ كَىْ نُسَبِّحَكَ كَثِيرًا ﴿٣٣﴾ وَنَذْكُرَكَ كَثِيرًا
﴿٣٤﴾ إِنَّكَ كُنتَ بِنَا بَصِيرًا ﴿٣٥﴾ قَالَ قَدْ أُوتِيتَ سُؤْلَكَ يَٰمُوسَىٰ ﴿٣٦﴾

Annabi Musa (AS) ya roƙi Allah cewa, *“Kuma Ka bani Waziri daga Ahali na. Haruna Dan-uwana. Ka karfafa halitta ta da shi. Kuma Ka shigar da shi cikin al-amari na. Domin mu yi tasbihin Ka da yawa. Kuma mu ambace Ka ambato mai yawa. Lallai Kai Ka kasance mai sani gare mu”.* Allah (SWT) Ya ce, *“Lallai ne an baka abin da ka roka ya Musa”.* (Taha:29-36)

Allahu Akbar! Annabi Musa ya roƙi Allah Ya ba ɗan-uwansa abubuwan da yake so ma kansa kuma Allah (SWT) Ya ba ko wannensu waɗannan abubuwa. Sai gashi su biyu duka sun zama Annabawa kuma Manzannin Allah. To, jama’ar Musulmi ga fa abin koyi, sai dai da wuya. Don Allah mu daure mu yi koyi da su da sauran

Annabawa da Sahabbai da manyan mutanen kirki wadanda ke son junansu.

Ya ‘yan-uwana, mu duba irin yadda Sahabban Manzon Allah (AS) suka so juna kuma Allah Ya saka masu da yin galaba a kan kafirai da ni’imomi na duniya da na lahira. Mu duba yadda Shehu Usman Danfodio da ɗan-uwansa Shehu Abdullahi da sauran na tare da su suka so juna kuma Allah Ya basu galaba a bisa sarakunan kasar Hausa da makwabtansu har suka kafa daular da ba’a taɓa yin irinta ba a wannan sashe na duniyarmu. A nan kusa-kusa, mu duba yadda su Sardaunan Sakkwato, Alhaji Sir Ahmadu Bello suka so junansu har suka kafa Arewacin Najeriya wadda a yanzu muke neman mu kafa irinta amma abin ya gagara.

Soyayya a cikin Musulunci tana da rassa da dama, amma ni a wannan wasiƙa na dauki rassa guda ukku kamar haka:-

1. Son Allah (SWT) da Manzonsa (SAW).
2. Son. Iyaye da Shugabanni
3. Son ‘Yan-uwa Musulmi

## Son Allah da ManzonSa

Ya ‘yan-uwana, tilas ne Musulmi ya so Allah (SWT) da ManzonSa (SAW). Dole wannan so ya zama a cikin zuciya da kuma a fili. Ka yarda da Allah da kuma abinda Ya saukar da shi ta hannun Annabi Muhammadu (SAW),

ka kuma yi biyayya ga umurnin Allah da na Manzonsa, shine cikakken soyayya ga Allah da Manzonsa kuma shine Musulunci. Yin akasin wannan shine kafirci kamar yadda Allah Ya ke cewa:-

وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَتَّخِذُ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَندَادًا يُحِبُّونَهُمْ كَحُبِّ ٱللَّهِۖ وَٱلَّذِينَ
ءَامَنُوٓاْ أَشَدُّ حُبًّا لِّلَّهِۗ

*Kuma akwai wasu mutane da ke riƙon abokan tarayya waɗanda ba Allah ba, suna son su kamar son Allah, Kuma waɗanda suka yi imani su suna tsananin son Allah.* (Baqara:165)

Bayani kuma ya zo mana a cikin Al-Qur'ani  cewa muddin muna son Allah, to sai mu bi Annabi Muhammadu (SAW). Ta wannan ne Allah zai so mu kuma Ya gafarta mana zunubbanmu kuma Ya yi mana rahama. Allah Ya na cewa:-

قُلْ إِن كُنتُمْ تُحِبُّونَ ٱللَّهَ فَٱتَّبِعُونِى يُحْبِبْكُمُ ٱللَّهُ وَيَغْفِرْ لَكُمْ ذُنُوبَكُمْۗ
وَٱللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ

*Ka ce, Idan kun kasance kuna son Allah, to, ku bi ni, Allah zai so ku kuma Ya gafarta maku zunubbanku. Kuma Allah mai gafara ne, mai jin-ƙai.* (Ali-Imran:31)

Ya kamata mu jaddada cewa son Allah da ManzonSa da bin abinda Allah Ya saukar ta hannun Manzon Allah (SAW) da yin abubuwan da Allah Ya ce a yi da kuma barin abubuwan da Allah Ya ce a bari, sune hanyoyin da zasu kaimu ga rahama da jinƙai na Allah (SWT).

Allah (SWT) Ya yi mana kashedi da riƙon wadanda suke son kafirci a kan imani su zama masoyanmu, ko da ya kasance waɗan nan masu son kafircin a kan imanin iyayenmu da matanmu da ‘ya-yanmu da ‘yan-uwanmu ne, kamar yadda Allah Ya ke cewa:-

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّخِذُوٓاْ ءَابَآءَكُمۡ وَإِخۡوَٰنَكُمۡ أَوۡلِيَآءَ إِنِ ٱسۡتَحَبُّواْ
ٱلۡكُفۡرَ عَلَى ٱلۡإِيمَٰنِۚ وَمَن يَتَوَلَّهُم مِّنكُمۡ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ﴿٢٣﴾ قُلۡ
إِن كَانَ ءَابَآؤُكُمۡ وَأَبۡنَآؤُكُمۡ وَإِخۡوَٰنُكُمۡ وَأَزۡوَٰجُكُمۡ وَعَشِيرَتُكُمۡ وَأَمۡوَٰلٌ
ٱقۡتَرَفۡتُمُوهَا وَتِجَٰرَةٞ تَخۡشَوۡنَ كَسَادَهَا وَمَسَٰكِنُ تَرۡضَوۡنَهَآ أَحَبَّ
إِلَيۡكُم مِّنَ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَجِهَادٖ فِي سَبِيلِهِۦ
فَتَرَبَّصُواْ حَتَّىٰ يَأۡتِيَ ٱللَّهُ بِأَمۡرِهِۦۗ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡفَٰسِقِينَ ﴿٢٤﴾

*Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku riƙi ubanninku da ‘yan-uwanku masoya idan sun nuna son kafirci a kan imani. Kuma waɗanda suka jiɓince su daga cikinku, sune azzulumai.*

*Ka ce: idan ubanninku da ɗiyanku da 'yan-uwanku da matanku da danginku da dukiyoyi waɗanda kuka yi tarinsu, da fatauci wanda kuke tsoron tasku gareshi da gidaje waɗanda kuke yarda da su, sun kasance mafi soyuwa a gareku daga Allah da Manzonsa, to ku jira har Allah Ya zo da umurninsa. Kuma Allah ba Ya shiryar da mutane fasiƙai.* (At-Tauba:23-24)

## Son Iyaye da Shugabanni

Ya 'yan-uwana Musulmi, soyayya a Musulunci tana tare da biyayya, don haka muddin kana son Allah da ManzonSa, tilas ne ka rika biyayya ga Allah da ManzonSa.

To, haka nan soyayya ga iyaye da shugabanni, a nan ma tilas ne kayi biyayya garesu. Amma fa, so da biyayya ga iyaye da shugabanni ya biyo bayan in suna yi maka umurni da abinda bai saɓa ma Allah da ManzonSa ba.

Kamar yadda muka riga muka karanta, duk wanda yayi maka umurni da yin abinda ya saɓa ma Allah (SWT) to bai halatta ba ka yi abin, domin bin Allah shi ke gaba.

A Musulunci, Shugaba ke koyarwa kuma ya tabbatar da bin dokokin Allah kuma ya tsaida hukunci. Ashe ya zama tilas a yi masa biyayya kamar yadda ya zama tilas shi Shugaban ya yi adalci.

Don haka, yin biyayya ga Shugaba (sarakuna, masu mulki, malamai da sauran magabata) wajibi ne muddin dai

biyayyar bata saɓa ma Shari’ah ba. Wannan umurni ne daga Allah (SWT) inda Ya ke cewa:-

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَ وَأُوْلِي
ٱلْأَمْرِ مِنكُمْۖ

*Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi biyayya ga Allah kuma ku yi biyayya ga Manzo da kuma waɗanda suka jiɓinci al-amurra daga cikinku (shugabanni)* (An-Nisaa:59)

Ya ‘yan-uwana, mu sani cewa Iyaye, matsayinsu na musamman ne kuma bin su da son su da kyautata masu ya zama tilas-ala-tilas. Allah (SWT) Ya ce:-

وَوَصَّيْنَا ٱلْإِنسَـٰنَ بِوَٰلِدَيْهِ إِحْسَـٰنًاۖ

*Kuma Mun yi wasiyya ga mutum game da mahaifansa biyu da ya kyutata masu* (Ahkaf:15)

وَوَصَّيْنَا ٱلْإِنسَـٰنَ بِوَٰلِدَيْهِ حُسْنًاۖ

*Kuma Mun yi ma mutum wasiyyar kyautatawa ga iyayensa* (Ankabut:8)

۞وَقَضَىٰ رَبُّكَ أَلَّا تَعْبُدُوٓا۟ إِلَّآ إِيَّاهُ وَبِٱلْوَٰلِدَيْنِ إِحْسَٰنًا ۚ إِمَّا يَبْلُغَنَّ عِندَكَ
ٱلْكِبَرَ أَحَدُهُمَآ أَوْ كِلَاهُمَا فَلَا تَقُل لَّهُمَآ أُفٍّ وَلَا تَنْهَرْهُمَا وَقُل لَّهُمَا
قَوْلًا كَرِيمًا ﴿٢٣﴾ وَٱخْفِضْ لَهُمَا جَنَاحَ ٱلذُّلِّ مِنَ ٱلرَّحْمَةِ وَقُل رَّبِّ
ٱرْحَمْهُمَا كَمَا رَبَّيَانِى صَغِيرًا ﴿٢٤﴾

*Kuma Ubangijinka Ya hukunta kada kuyi bauta sai gareShi, kuma game da mahaifa biyu ku kyautata masu, kyautatawa, ko dai ɗayansu ya kai ga tsufa a gurinka ko dukkansu biyu, to, kada ka ce masu "tir", kuma kada ka yi masu tsawa, kuma ka fada masu magana mai karamci.*

*Kuma ka sassauta masu fikafikan tausayawa na rahama. Kuma ka ce "Ya Ubangijina, Ka yi masu rahama kamar yadda suka yi renona ina karami"* (Isara'i:23-24)

Ya ku Iyayenmu, ku tuna cewa 'ya-'yanku suna da hakkin reno da ilmantarwa da sauransu a kan ku, kamar yadda Allah Ya yi umurni. Allah (SWT) Ya yi mana umurnin kare kawunanmu da na iyalanmu daga azabar wutar lahira, don haka ya zama wajibi garemu mu so iyalanmu kuma mu yi masu tarbiyya irin ta Musulunci. Allah Yana cewa:-

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ قُوٓا۟ أَنفُسَكُمْ وَأَهْلِيكُمْ نَارًا وَقُودُهَا ٱلنَّاسُ
وَٱلْحِجَارَةُ عَلَيْهَا مَلَٰٓئِكَةٌ غِلَاظٌ شِدَادٌ لَّا يَعْصُونَ ٱللَّهَ مَآ أَمَرَهُمْ وَيَفْعَلُونَ
مَا يُؤْمَرُونَ

*Ya ku waɗanda suka yi imani, ku kare kawunanku da iyalanku daga wata wuta wadda makamashinta, mutane da duwatsu. A kanta akwai wasu Mala'iku masu kauri da tsananin karfi. Basu saɓa wa Allah ga abinda Ya umurcesu, kuma suna aikata abinda ake umurninsu.* (Tahrim:6)

### Son 'Yan-uwa Musulmi

Ya 'yan-uwana, bayan so da biyayya ga Allah (SWT) da ManzonSa (SAW) da Iyaye da Shugabanni a cikin mu, sai mu karkata soyayyarmu zuwa ga sauran 'yan-uwa Musulmi. Su kuma abokan zamanmu wadanda ba Musulmi ba, sai mu basu hakkinsu kamar yadda Allah Ya shimfiɗa. Ga abinda Allah (SWT) Ya ke cewa game da soyayya da hadin kai tsakanin Musulmi:-

وَٱعْتَصِمُوا۟ بِحَبْلِ ٱللَّهِ جَمِيعًا وَلَا تَفَرَّقُوا۟ ۚ وَٱذْكُرُوا۟ نِعْمَتَ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ إِذْ
كُنتُمْ أَعْدَآءً فَأَلَّفَ بَيْنَ قُلُوبِكُمْ فَأَصْبَحْتُم بِنِعْمَتِهِۦٓ إِخْوَٰنًا وَكُنتُمْ عَلَىٰ
شَفَا حُفْرَةٍ مِّنَ ٱلنَّارِ فَأَنقَذَكُم مِّنْهَا ۗ كَذَٰلِكَ يُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمْ ءَايَٰتِهِۦ لَعَلَّكُمْ
تَهْتَدُونَ

*Ku riƙe igiyar Allah gaba ɗayanku kuma kada ku rar-rabu. Kuma ku tuna ni'imar Allah a kanku lokacin da kuka kasance abokan gaba sannan Ya haɗa zukatanku da soyayya sai kuka wayi gari 'yan-uwan juna da ni'imarsa. A da can kuwa kun kasance a kan gaɓar ramin wuta,*

*sannan Ya tsamo ku daga gareta. Kamar haka ne Allah Ya ke bayyana maku ayoyinsa don ku shiriya.* (Ali-Imran:103)

To ‘yan-uwana, wannan fa umurni ne daga Mai-kowa Mai-komi Allah Madaukaki. Mu riƙe igiyar Allah, kada mu rar-rabu. Mu tuna Musulmin farko maƙiyan juna ne kuma sun ginu a bisa kafirci amma Allah Ya tsamo su, Ya sanya masu soyayyar juna kuma Ya mayar da su cikin Musulunci. A da can a matsayin kafirai suna bisa gaɓar fadawa wutar lahira sai ya tsirad da su zuwa gaɓar shiga Aljannah. Don haka ya rage namu ko mu koma gaɓar wuta mu tsunduma cikinta, ko mu tsaya a gaɓar Aljannah mu shiga cikinta. Allah Ya sanya mu hanya madaidaiciya mai kaimu Aljannah, ameen. Amma mu tuna fa wannan addu’a bata cika sai da aiki. Tilas mu bi umurnin Allah na riko da igiyar Musulunci ta so da bin umurnin Allah da ManzonSa da soyayya da biyayya ga iyaye da shugabanni da soyayya da haɗin kai ga sauran Musulmi.

Ya ‘yan-uwana, shin me ke hana mu zama cikakkun Musulmi, mu riƙa son juna da hada kawunanmu maimakon yin ƙiyayya da hassada? Allah (SWT) Ya bamu amsa da cewa son duniya da abubuwan ƙawa na cikinta shine babban abinda ke haddasa mana gaba da hassada. Kuma Allah (SWT) Ya yi mana albishir da cewa lahira (Aljannah), tafi kuma ita ce abinda Musulmin kirki zai duƙufa wajen nema. Allah Ya ce:-

زُيِّنَ لِلنَّاسِ حُبُّ ٱلشَّهَوَٰتِ مِنَ ٱلنِّسَآءِ وَٱلْبَنِينَ وَٱلْقَنَٰطِيرِ ٱلْمُقَنطَرَةِ مِنَ
ٱلذَّهَبِ وَٱلْفِضَّةِ وَٱلْخَيْلِ ٱلْمُسَوَّمَةِ وَٱلْأَنْعَٰمِ وَٱلْحَرْثِ ۗ ذَٰلِكَ مَتَٰعُ ٱلْحَيَوٰةِ
ٱلدُّنْيَا ۖ وَٱللَّهُ عِندَهُۥ حُسْنُ ٱلْمَـَٔابِ ﴿١٤﴾ ۞ قُلْ أَؤُنَبِّئُكُم بِخَيْرٍ مِّن ذَٰلِكُمْ ۚ
لِلَّذِينَ ٱتَّقَوْا۟ عِندَ رَبِّهِمْ جَنَّٰتٌ تَجْرِى مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا
وَأَزْوَٰجٌ مُّطَهَّرَةٌ وَرِضْوَٰنٌ مِّنَ ٱللَّهِ ۗ وَٱللَّهُ بَصِيرٌۢ بِٱلْعِبَادِ ﴿١٥﴾ ٱلَّذِينَ
يَقُولُونَ رَبَّنَآ إِنَّنَآ ءَامَنَّا فَٱغْفِرْ لَنَا ذُنُوبَنَا وَقِنَا عَذَابَ ٱلنَّارِ ﴿١٦﴾

*An kawata ma mutane son sha'awa daga mata da 'ya'ya da dukiyoyi abubuwan tarawa daga zinariya da azurfa, da dawaki kiwatattu da dabbobin da ake ci da hatsi. Wannan shine daɗin rayuwar duniya. Kuma Allah a wurinsa kyakkyawar makoma take.*

*Kace: Shin ingaya maku mafi alheri daga wannan? Akwai gidajen Aljannah a wurin Ubangiji saboda waɗanda suka bi shi da takawa, koguna suna gudana daga ƙarƙashinsu, suna madawwama a cikinsu, da matan aure tsarkakakku, da yarda daga Allah. Kuma Allah mai gani ne ga bayinsa.*

*Waɗanda suke cewa, Ya Ubangijinmu. Lallai ne mu mun yi imani, ka gafarta mana zunubbanmu kuma ka tsirar damu daga azabar wuta*. (Ali-Imran:14-16)

Ashe abin mai wuya ne kuma mai sauƙi. Wuyarsa ita ce shin muna iya daurewa mu so lahira fiye da duniya? Abin

yi anan shine mu tashi tuƙuru mu yi ta ibada da tsare dokokin Allah domin mu samu lahira mai kyau kuma mu yi sana'a domin samun rayuwar duniya mai kyau. Sauƙin abin shine, muddin dai muna gudanar da rayuwarmu kamar yadda Allah Ya ce, to zamu samu rayuwa a duniya mai amfani kuma mu samu shiga Aljanna in ajalinmu ya zo.

Manzon Allah (SAW) ya yi mana bayanin yadda zamu gane Musulmi masu son juna da kuma alherin da ke tattare da wannan soyayya kamar haka:-

Nu'uman bin Bashir (RA) ya ce, Manzon Allah SAW) yana cewa:-

*Zaka ga waɗanda suka yi imani suna tausaya wa juna, suna son juna, suna yi ma juna kirki, tamkar jikin mutum ɗaya, wanda idan wani sashe baya lafiya to sai sauran sassan su kama zazzabi da rashin barci.* (Bukhari kashi na 8, hadisi na 40)

Anas bin Malik (RA) ya ce:-

*Wani mutum ya tambayi Manzon Allah (SAW) cewa, "yaushe ne za'a yi tashin kiyama?" Sai Annabi ya ce, "Me ka shirya mata?" Sai mutumin ya ce, "Ban shirya mata ba sosai wajen Sallah, Azumi da sadaka, amma ina son Allah da Manzonsa". Sai Annabi ya ce masa, "Mutum yana tare da wanda ya ke so (a ranar lahira)"* (Bukhari, kashi na 8, hadisi na 19

## Haza Wassalam

Ya ‘yan-uwana Musulmi, ya kamata mu ba kawunanmu magana mu so juna mu zama tsintsiya maɗaurinki ɗaya kamar yadda Allah (SWT) Ya yi mana umurni. Wannan shine zai fitar damu daga ƙangin da muke ciki. Ya kamata:-

1. Mu so Allah (SWT) da ManzonSa (SAW) kuma mu yi ibada da gudanar da rayuwa kamar yadda Allah (SWT) Ya yi mana umurni. Wannan shine zai kaimu ga samun alherin Allah a duniya da lahira.

2. Mu so, kuma mu girmama iyayenmu da shugabanninmu, kuma mu yi masu biyayya kamar yadda Shari’ah ta shinfida. Su kuma su yi mana adalci kamar yadda Allah Ya umurcesu. Wannan shine zai sanya mu samu jagoranci na gari wanda zai kaimu ga nasara.

3. Mu so junanmu, mu bar gulma, da hassada da kafirta junanmu. Idan har waninmu ko wasunmu suna barna, to Allah Ya nuna mana yadda zamu yi masu wa’azi da nasiha ba tare da wulaƙanci ko tozartawa ba, kamar haka:-*Ka yi kira zuwa ga hanyar Allah da hikima da wa’azi mai kyau* (An Nahl:125)

4. Mu ba maƙwabta da abokan zamanmu, ko da ba Musulmi bane, duk haƙƙinsu kamar yadda Allah Ya shinfida mana. Wannan shine zai sanya su girmama mu, su riƙa sha’awar addininmu (wata ƙila ma su shigo) kuma

su riƙa zama lafiya da mu kamar yadda Manzon Allah (SAW) ya yi zaman lafiya da waɗanda ba Musulmi ba.

Zan rufe wannan wasiƙa tawa da kawo abin da Allah (SWT) Ya ce da abin da ManzonSa (SAW) ya ce game da Musulmi masu son juna:-

An ruwaito a cikin Hadisi Qudsi, na 23, cewa a ranar tashin kiyama Allah (SWT) zai ce:-

*Ina waɗanda suka so junansu domin haskakani? A yau zan yi masu inuwa a cikin inuwa Ta, kuma yau rana ce da babu inuwa sai Tawa.*

An ruwaito a cikin Al-Muwatta, kashi na 47, hadisi na 16, cewa, Abdullah al-Khurasani ya ce, Manzon Allah (SAW) yana cewa:-

*Idan kuka gaisa da hannuwanku to ƙiyayya zata gushe, kuma idan kuka so junanku to gaba zata ɓace.*

Al-Tirmidhi ya ruwaito a hadisi na 1350, cewa Sahl ibn Sa'ad ya ce, wani mutum ya zo wajen Manzon Allah (SAW) ya tambaye shi cewa:-

*"Ya Manzon Allah, ina son ka nuna mani abinda zan yi Allah Ya so ni kuma mutane su so ni" Sai Manzon Allah ya ce masa, "In ka guji Duniya to Allah zai so ka kuma idan ka guji abin hannun mutane to mutane za su so ka"*

Ya 'yan-uwana, muddin dai muna son mutum ko wani abu wanda ba mutum ba, to ba zamu so wani abu na rashin jin daɗi ya same shi ba. Don haka mu ƙarfafa soyayyarmu

kuma mu kare junanmu daga sharri da mugunta. Mu jarraba son juna da tsaida adalci mu ga idan wani yana iya karyamu.

Da fatan cewa Allah (SWT) zai yi mana muwafaƙa da alhairansa, nake cewa,

Wassalamu Alaikum

**Prof. Sani Abubakar Lugga, MFR**
**Wazirin Katsina**